## Su Wa Ke Cikin Ahlul-Bait ?

An nuna cewa Iyalan Annabi (s) - wadanda akan kira da *Ahlul-bait* da *'Itrah* da *Aal* - sun hado Fatima al-Zahra, da mijinta, da `ya`yansu Imam Hassan da Imam Hussaini (a). Wannan iyali na mutum biyar tare da Manzon Allah (s) a matsayin shugabansu su suke raye raye a lokacin da aka saukar da ayoyin AlKur'ani masu bayani a kan darajojinsu ga Annabi (s). Ko ta halin kaka dai, sauran Imamai tara daga jikokin Hussaini (s) suma kebabbun Iyalan ne, na karshen su shi ne Imam al-Mahdi (a). Annabi (s) ya ce:

- "Ni da Ali da Hasan da Husayn da **tara daga jikokin Hussaini** tsarkaka ne kuma wadanda ba sa kuskure." [al-Juwayni, *Fara'id al-Simtayn*, (Beirut, 1978), shafi na 160. a lura da cewa girman matsayin al-Juwaini a fagen ilimin hadisi ya tabbata a wajen Zahabi a cikin *Tazkiratul-Huffaz*, juz'I na 4, shafi na 298; da wajen Ibn Hajar al-'Asqalani s cikin *al-Durar al-Kaminah*, juz'i na 1, shafi na 67.]
- "Ni ne shugaban Annabawa, kuma Ali ibn Abi Talib shi ne shugaban Wasiyyai, kuma bayana Khalifofi goma sha biyu za su kasance, wadanda na farkonsu shi ne Ali ibn Abi Talib na karshen su kuma shi ne al-Mahdi." [al-Juwaini,*Faraid al-Simtayn*, shafi na 160]
- "Mahdi daya ne daga cikin mu **Ahlul-Bait**"and"Mahdi zai zama daga iyalaina, daga jikokin Fatima"[Ibn Ibn Majah, *al-Sunan*, juz'i na2, shafi na 519, lamba na 4085-6; Abu Dawud, *al-Sunan*, jiz'i na 2, shafi na 207]

## To Matan Annabi (s) Fa ?

Ayar tsakakewa "*Lallai Allah na nufin ...* " ta sauka ne ga Annabi (s) a lokacin yana dakin matarsa Ummu Salama (Allah Ya yarda da ita); sai Annabi ya kira Hasan da Husaini da Fatima da Ali, sai ya hada su tare ya rufe su da mayafi, sannan y ace: "**Ya Allah, wadannan su ne Ahlul-Baiti na, don haka Ka kawar da duk wani rashin datti daga Ahlul-Baiti na, Ka kuma tsarkake su cikakken tsarkakewa**." sai Ummu Salma ta ce: "Annabi, ko ina tare da su?" Sai Annabi (s) ya ce: "**Ki tsaya a inda kike kuma kina tare da alheri**."

- al-Tirmidhi, *al-Sahih*, juz'i na 5, shafi na 351 da na 663
- al-Hakim al-Naysaburi, *al-Mustadrak `ala al-Sahihayn*, juz'i na 2, shafi na 416. Har ya yi bayani da cewa hadisin *sahih* ne bisa ka'idar Bukhari
- al-Suyuti, *al-Durr al-Manthur*, juz'i na 5, shafi na 197

Farkon surar ta 33 a aya ta 33 da bayanan da suka biyo bayan ta suna magana ne da matan Annabi (s) da dalilin amfani da lamirin magana da mata. Amma a ayar tsarkakewa, sai yanayin magana ya canza zuwa lamiri mai nuna magana da maza ko taron maza da mata. Wannan na nuna cewa ita (ayar) a kashin kanta ta sauka ne kan wasu mutane daban.

**Don samun karin bayani a kan sahihiyar fassarar Msulunci, kamar yadda Ahlul-Baiti suka yi bayani, tuntubi wannan adreshi ta yanar-gizo:**

**http://al-islam.org/faq/**

*v1.0*

*Lallai Allah na nufin kawar da duk wata dauda daga gare ku, ya ku `yan-gidan Annabi* **(Ahlul-Bait)** *ya kuma tsarkake ku cikakken tsarkakewa*
[Ayar Tsarkakewa daga AlKur'ani, 33:33]

Sahabbai sun tambayi Annabi Muhammad (s) cewa:
"Ya ya za mu yi maka salati?"... Sai ya ce:
"Ku ce: '*Ya Allah! Ka yi tsira ga Muhammadu da Iyalan Muhammadu, kamar yadda Ka yi tsira ga Ibrahim da Iyalan Ibrahim, lallai kai ne Abin yabo kuma Mai baiwa.*'"
[*Sahih al-Bukhari*, juz'i na 4, littafi na 55, lamba na 589]

# Me Yasa Za A Bi 'yan gidan Annabi (s)?

`Yan Shi'a sun yi imani da cewa abubuwa biyu da Manzon Allah (s) ya bari su ne AlKur'ani da *Ahlul-Baiti* (wasu kebabbu daga iyalansa). *Ahlul-Baiti* su ne mabubbugar ingantacciyar *Sunnar* Manzon Allah (s). Da karbar dokoki daga ***duk*** wadannan cibiyoyi biyu ne kawai Musulmi zai sami fatan samun shiriya na gaskiya.

## Abubuwan Da Annabi Muhammadu Ya Bari

**"Na kusa amsa kira (na mutuwa). Lallai ni mai barin nauyaye biyu (*thaqalaini*) ne a cikin ku: Littafin Allah da Ahlul-Bait dina. Hakika su biyun ba za su taba rabuwa har lokacin da za su same ni a bakin tafki."**

Wannan ingantaccen *hadisi* na Annabi Muhammadu (s), sama da Sahabbai 30 ne suka riwaito shi, kuma malaman Ahlusunna masu yawan gaske sun nakalto shi. Wasu daga mashahuran hanyoyin wannan *hadisi* sun hada da:

- al-Hakim al-Naysaburi, *al-Mustadrak `ala al-Sahihayn* (Beirut), juz'i na 3, shafi na 109-110, da na 148, da na 533). Har ma ya yi bayanin cewa hadisin *sahih* ne bisa ka'idar Bukhari da Muslim; Zahabi kuma ya tabbatar da hukuncin na shi
- Muslim, *al-Sahih*, (Fassaran turanci), littafi na 031, lamba na 5920-3
- al-Tirmidhi, *al-Sahih*, juz'i na 5, shafi na 621-2, lambobi na 3786 da na 3788; da juz'i na 2, shafi na 219
- al-Nasa'i, *Khasa'is'Ali ibn Abi Talib*, hadisi mai lamba 79
- Ahmad b. Hanbal, *al-Musnad*, juz'i na 3, shafi na 14, da 17 da na 26; da juz'i na 3, shafi na 26 da na 59; da juz'i na 4, shafi na 371; da juz'i na 5, shafi na 181-2, da na 189-190
- Ibn al-'Athir, *Jami` al-'usul*, juz'i na 1, shafi na 277
- Ibn Kathir, *al-Bidayah wa al-nihayah*, juz'i na 5, shafi na 209. Ya ciro zancen Zahabi na tabbatar da *ingancin* wannan *hadisin*.
- Ibn Kathir, *Tafsir al-Qur'an al-'Azim* , juz'i na 6, shafi na 199
- Nasiruddin Albani,*Silsilatul-Ahadith al-Sahihah* (Kuwait); al-Dar al-Salafiyya), juz'i na 4, shafi na 355-8. Inda ya lissafo isnadai masu yawa da ya yarda da amincinsu.

Akwai wasu hanyoyi masu ya na wannan *hadisi* da ba zai yiwu a kawo su a nan ba.

## Kenan Annabi (s) Bai Fadi Cewa: "Na Bar Muku AlKur'ani Da Sunnah A Baya na Ba" ?

Wannan sanannen kuskure ne. Gaskiyan al'amari shi ne cewa babu wata amintacciyar madogara ga wannan zance da aka dangana shi ga hudubar Annabi (s) ta karshe **Kwata kwata ba shi a daya daga cikin litaffan *Sihah* din nan shida!!** Kuma wanda ya zo a *Muwatta'* na Maliki, da *Siratu Rasul Allah* na Ibin Hisham, wanda daga gare shi ne Tabari ya riwaito a *Ta'rikh*, **duk suna fama da karayar isnadi**, inda ake samun gibin isnadi da yawa! Sauran hanyoyin kuma da suke da cikakkun hanyar riwaya (*isnad*) - wadanda kadan ne kwarai - **duk sun kunshi masu riwayar da ka dace da tsananin rauninsu** a wajen manyan malaman *rijal*. na Ahlusunna. Masu sha'awar bin diddigi da bincike na iya komawa littafan da suka kebi wannan fanni don tabbatar da wadannan kwararan dalilai.

A bayyane take cewa babu wanda ke ganin cewa kar a bi *Sunnar* Annabi (s). Kamar yadda aka bayyana a baya, Annabi (s) na son ganin Musulmi sun koma ga Ahlul baiti ne a matsayin amintacciya kuma tsarkakkar hanya`r da ba kuskure zuwa *Sunnah*.

## Menene Abu Na Musamman Game Da `Yan-Gidan Annabi (s) ?

Lokacin da aya nan: *"Ka ce (ya kai Muhammad): 'ba na tambayar ku wani lada a kan wannan (aikin isar da sakon Allah) face kaunar makusanta."'* (42:23) was ta sauka, sai Musulmi suka tambayi Annabi cewa: "Su wanene wadannan makusantan naka da kaunarsu ta wajaba a kan mu?" **Sai Ya amsa da cewa: "Ali, da Fatima da `ya`yansu biyu."**"

- al-Hakim al-Naysaburi, *al-Mustadrak `ala al-Sahihayn*, juz'i na 2, shafi na 444
- al-Qastallani, *Irshad al-Sari Sharh Sahih al-Bukhari*, juz'i na 7, shafi na 331
- al-Suyuti, *al-Durr al-Manthur*, juz'i na 6, shafi na 6-7
- al-Alusi al-Baghdadi, *Ruh al-Ma'ani*, juz'i na 25, shafi na 31-2

AlKur'ani ya kara tabbatar da wannan matsayi na gaskiya da darajojin Ahlul-Baiti, a lokacin da ya ja da Kiristocin Najiran. Lokacin da ayar: "*Kuma duk wanda ya yi jayya da kai a kan wannan al'amari (na haihuwar Annabi isa ba uba) bayan abin da ya zo maka na ilimi (yakini), sai kace: ku zo mu kira `ya`yanmu da `ya`yanku da matanmu da matanku da (wadanda suka fi kusa da) mu da (wadanda suka fi kusa da) ku, sannan mu yi tsinuwa, mu roki la'anar Allah a kan makaryata.*" (3:61) ta sauka, **Annabi (s) ya kira Ali, da Fatima, da Hassan da Hussaini sannan ya ce: 'Ya Allah, wadannan su ne Iyali(*Ahli*) na**'.

- Muslim, *al-Sahih*, (Fassaran Turanci), littafi na 031, lamba na 5915
- al-Hakim al-Naysaburi, *al-Mustadrak `ala al-Sahihayn*, juz'i na 3, shafi na 150. Ya kuma bayyana cewa shi *sahih* ne a bisa ka'idar Bukhari da Muslim
- Ibn Hajar al-'Asqalani, *Fath al-Bari Sharh Sahih al-Bukhari*, juz'i na 7, shafi na 60
- al-Tirmidhi, *al-Sahih*, kitab al-manaqib, juz'i na 5, shafi na 596
- Ahmad b. Hanbal, *al-Musnad*, juz'i na 1, shafi na 185
- al-Suyuti, *Tarikh al-Khulafa'*, (London, 1995), shafi na 176

## To Nuna Girmamawa ga Ahlul-Baiti Kawai Bai Wadatar ba ?

Girmama AlKur'ani kawai ya wadatar? Ba shakka Musulmi ba su da wani zabi da ya wuce bon shi, a matsayin shi na wajen samun shiriya, a *duk* harkokinsu. Annabi (s) ya barwa Musulmi nauyaye biyu, kuma ya yi alkawarin cewa ba za su taba rabuwa ba har ranar kiyama. **Jona Ahlul-Baiti da AlKur'ani da Annabi (s) ya yi, yana son ya gaya mana ne cewa ba kawai girmama su wajibi ba ne, a'a har ma da daukar bayanan *akidar* Musulunci da *furu'a* da *hadisi* da *tafsiri* daga gare su.**

**"Ku Saurara! Ahlul-Baiti Dina Kamar Jirgin Nuhu Ne. Wanda Ya Rike Shi Ya Tsira, Wanda Kuwa Ya Kau Da Kai Daga Gare Shi Ya Halaka"**

- al-Hakim al-Naysaburi, *al-Mustadrak `ala al-Sahihayn*, juz'i na 3, shafi na 151; da juz'i na 2, shafi na 343. Ya kuma bayyanna cewa shi *sahih* ne bisa ka'idar f Muslim
- al-Suyuti, *al-Durr al-Manthur*, juz'i na 1, shafi na 71-72
- Ibn Hajar al-Makki, *al-Sawa'iq al-Muhriqa*, shafi na 140. Ya bayyana cewa wannan hadisin an riwaito shi ta hanyoyi da yawa, wadanda sashensu na karfafa sashe.